## ABOUT CITAD

CITAD (www.citad.org) is a capacity building Civil Society Organization whose activities covers Research, Advocacy, Training and Publicity in all areas of ICTs.
Its vision is; a Knowledge-based Democratic Society free of Hunger while its Mission is; Using ICTs to Empower Citizens for a just and knowledge-based Society that is anchored on sustainable and balanced development.


**MAIN OFFICE:**
3rd Floor, NISTF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 0800-68078282, 080-54362931, 070-33427467
• E-mail: info@citad.org, Citadev@gmail.com, citad4peace@citad.org, Website: www.citad.org, www.citad4peace.org.ng

**BAUCHI OFFICE:**
NUJ Secretariat, Opposite Reinsurance House, Ahmadu Bello Way, Bauchi State.
GSM: 08064867312


CITAD

actionaid

UKaid from the British people

# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN GARIN SAJI





*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD) Tare Da Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**

CITAD

*A Knowledge-Based Democratic Society Free of Hunger*

# ABUBUWAN DA KE CIKI

KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN SAJI2

Jadawali....................................................................................................................i

Godiya.......................................................................................................................ii

Gabatarwa..................................................................................................................1

Manufa.......................................................................................................................1

Tsarin da aka yi amfani da shi...................................................................................2

Cikakken Bayani Game Da Garin Saji......................................................................4

Tarihin Garin  Saji.....................................................................................................7

Taswirar Garin Saji....................................................................................................7

Yanayin Zamantakewa..............................................................................................10

Ilimi..........................................................................................................................11

Juyawar Yanayi.........................................................................................................12

Tantance Haƙƙoƙin Mata..........................................................................................18

Take Haƙƙoƙin.........................................................................................................20

Kalubalen Da Ke Fuskantar Unguwar  Saji A Halin Yanzu.....................................23

Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli.............................................26

Kungiyoyi da mutanen da za su iya tallafaw...........................................................28

Tantance Karfin ikon kawo Cangi............................................................................30

Tantance Hadura dake barazane ne ga jama'ar Saji................................................32

Tantance Hanyoyin Samun Bayanai.........................................................................33

Tsarin Da Za A Bi Domin Warware Matsalolin......................................................33

# GODIYA

Wallafawar wannan littafi yasamu yiwuwane tareda tallafi daga Sashin Kula da Cigaba na ƙasa da ƙasa na Gwamnatin Birtaniyya (DFID ta hannun ƙungiyar ActionAid Nigeria (AAN). Dole ne a yabawa wannan Cibiya ta ActionAid saboda jajircewa ta wajen Bunƙasa Demokuraɗiyya ta hanyar wayar  da Jama'a su fahimci Demokuraɗiya.

Muna godiya ta musamman ga Shugaban Cibiyar Fasahar Sadarwa da Ci gaban Al'umma (CITAD), Y.Z. Ya'u domin kasancewarsa jigo wanda ya bada gudummawa ga kammaluwar wannan Littafi.

Godiyar mu bazata cikaba sai mun yaba da Kyakkyawar fahimta da hadin kai da ma'aikatan CITAD. Haka kuma mun yabawa da ƙoƙari da himmar Malam Ahmad AbdullahiYakasai, da Isyaku Garba' da Abubakar Auyo da Mukhtar Sulaiman Umar da Abdullahi Jido da Harira Abdulrahman wanda suka hana kansu hutu domin tabbatar da kammaluwar  wannan Kundi.

Muna miƙa cikakkiyar godiyarmu ga 'Yan kwamitin aiwatar da kundin wannan Gari na Zinyau da Mai Gari da Dagaci da kuma dukkannin waɗan da suka tallafa wajen gudanar da tsarin shirin wannan kundi, babu shakka zai ingan ta shirin nan gaba.





## TSARIN DA ZA A BI DOMIN WARWARE MATSALOLIN

Aƙarshen tattaunawar, an fitar da ƙwaƙƙwaran da za a bi domin warware matsalolin da aka gano ta hanyar yin amfani da gudummawar kowa da kowa da wasu dabaru domin tantance abubuwan da ke ci waal'ummar unguwar Garin Saji tuwo a ƙwarya. Abin da ke biye tsari ne na ayyukan da za aiwatar domin ganin mafarkin unguwar ya zama gaskiya.


| MUHIMMAN ABUBUWA | HANYAR DA AKA TSARA | LOKACI | MASUYIN AIKIN | ABUBUWAN DA AKE BUQATA | ABINDA KA IYA KAWO CIKAS | HUJJAR SAMUN NASARA |
|---|---|---|---|---|---|---|
| Ziyartar wasu rukunonin Al'umma a Saji | Ziyara ta kai tsaye | Sati 2 (15 zuwa 30 Disamba 2015) | CITAD da Kwamitin kundinSaji | • Brief of the project<br>• Mapping the groups | •Aikin Gona<br>•Zirga-zirga<br>•Kuɗaɗen isar da bayanai | Rahoton yan Kwaminti |
| Rubutaccen bayani game da CDC | Gabatarwa da karɓar shawarwari | Sati 2 30 Nuwamba | CITAD da Kwamitin kundinSaji | Rubutaccen bayani game da CDC | Lokaci da Kayan aiki | Kammalallen Kundin CDC |
| Kaddamarwa Kundin Saji CDC | Inɓitations Liaising with media | Jan 2016 | CITAD da Kwamitin kundinSaji | Rubutaccen bayani game da CDC | Lokaci da Kayan aiki | Ranar Kaddamarwa |
| Ziyarar ƙarfafa gwiwa ga waɗanda nauyi ya hau kansu | Planning meeting Ziyarce ziyarcen | Jan 2016 | CITAD da Kwamitin kundinSaji | Kwafi na Kammalallen Kundin CDC | Bayan ƙaddamarwa Fabairu. 2016 | Jagircewa |

Karin Haske: Wannan tsarin na watanni shida ne. An tsara shi ta yadda za a rinƙa sabunta shi duk lokacin da aka aiwatar da wani aiki a cikin abubuwan da aka shirya gudanarwa



WANI KWARI DA JAMAR SAJI KE SAMUN RUWAN AMFANI NAY AU DA KULLUN (YANA GUBATA)

Dagaci da masu unguwanni su ne masu magana da yawun al'umma garin, kuma suna da ƙarfin iko fiye da kansilan da aka zaɓa.








# GABATARWA

Wannan kundi na cigaban wannan garin yana ɗauke da gabaɗayan bayanai filla-filla da kuma taƙaitattun abubuwan da suka shafi Garin Saji da ke ƙaramar hukumar Rano a jihar Kano a tarayyar Najeriya. Wannan kundi zai zamawata madogara na yin izna wajen tabbatar da gaskiyar al'amura ga jama'ar Saji. Kundin yayi cikakken bayanin Garin da mutanenta da kuma albarkatun ƙasa da Allah Ya huwace mata.An tattaro waɗannan bayanai ne daga wajen wasu keɓantattun mutane mazauna Garin ta hanyar yin amfani da tsarin waiwaye adon tafiya domin yin bitar abubuwan da suka gudana da kuma tsarin nan na Action Aid wanda ke baiwa kowa damar bayar da gudummawa don tattara faɗakar da mutane sanin muhimmancin kowa ya shiga a dama da shi a al'amuran zaɓe wanda aka fi sani da (SCEEP).

Tsarin zai zama wani ginshiƙi na aiki tare da wasu garuruwan a ƙoƙarin saita al'umma kan gwadaben da za su rinƙa bibiyar abubuwan da gwamnatoci da wakilansu ke gudanarwa. Haka kuma, wannan kundin zai samar da wata kafa ta yin aiki tare tsakanin al'ummar garin da waɗanda suka zaɓa zuwa matakai daban-daban. An samar da kundin ne ta bin managartan tsare-tsare da wannan ƙungiya ta yi a baya, aka tattaro ƙwararru suka yi aiki ƙarƙashin inuwa ɗaya.

Hanyar amfani da tsarin waiwaye adon tafiya na yin amfani da cikakken bincike kamar binciko dangantakar mahukunta da haƙƙoƙin al'umma musamman mata da gano abubuwan da ke yi wa gain barazana da binciko ƙungiyoyi da mutanen da za su iya tallafawa da fahimtar hanyoyin sadarwa da al'ummar garin ke amfani da su da kuma matsalolin da suke ci musu tuwo a ƙwarya.

Domin cimma nasara abubuwan da aka ambata a sama, ActionAid ta aiwatar da tsarin waiwaye adon tafiya a garin. Ta amfani da sassa bakwai na tsarin tantancewar bayanai.Bayanan da aka tattara za su zama ginshiƙi na ƙarfafa gwiwa wanda zai ciyar da garin gaba yadda ake buƙata.

MANUFA

Manyan manufofin wannan kundi su ne kamar haka:

- Gano tare da adana al'amuran da suka shafi garin tare da fitar da wani tsari na shigo da al'ummar yankin don yin aiki tare.
- Zaburar da al'umma wajen neman abubuwan ci gaban garin daga wakilansu a ɓangarori daban-daban.
- Tallata ƙwarewa da ilimi da kuma abubuwa da Garin Saji ke fatan samu a dunƙule domin samun sauƙin bibiya.

HANYOYIN DA AKA YI AMFANI DA SU

Hanyoyin da aka bi wajen aiwatar da aikin sun haɗa da:

- Tattaunawa tun a karon fari tsakanin dattawan Gawuna da CITAD.
- Ziyarce-Ziyarce: An ziyarci wurare daban-daban tare da ganawa da mutanen na garin na tsawon kwanaki domin samun cikakkun bayanai na ɓangarori bakwai na wai waye adon tafiya (Reflection Action).
- Taron tantancewa da rubuta rahoton abubuwan da aka gano.

TSARIN DA AKA YI AMFANI DA SHI

- An yi amfani da abubuwa daban-daban wajen tantance ɓangarori bakwai nawai waye adon tafiya (Reflection Action).
- An yi amfani da taswira wajen binciko matsalolin da ke addabarr.
- An yi amfani da jerin gwanon haƙƙoƙi ɗan'adam wajen gano haƙƙoƙin al'ummar garin Saji.
- Jera abubuwa mafi sauƙi ya taimaka wajen tsara al'amuran da suka fi muhimmanci bi da bi waɗanda al'ummar garin suka gano.
- An yi amfani da bishiyar-matsaloli domin fahimtar abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu da kuma tattaunawa mai zurfi a kansu.





| Lamba | Hadura | Abinda ke Kawosu | Tasirin/Yadda Abin Yake Gudana | Wanda Yafi shafa |
|---|---|---|---|---|
| **1.** | - Gurɓacewar Ruwan sha | Karancin ingantaccen ruwan sha, | -Cututtuka kamar su Taifod | Dul al'umma |
| **2.** | Rigima tsakanin Manoma da Makiyaya | Karancin bayanai da wayar da kai | Asarar rayuka da dukiyoyi | Manoma |

Haɗarin gurɓacewar ruwa shine babbar haɗari a garin saji. Wannan ya afkune sakamakon ƙarancin ingantaccen ruwan sha wanda ke haifar da ɓarkewar cututtuka musamman zazzaɓin taifot wanda ka iya shafar kowa yaro ko babba a kowanne jinsi, wannan ya faruwa ne kowanne lokacin a cikin shakara. Mutane da dabbobi na shan ko amfani da idon ruwa tare kaitsaye.

Haɗari na biyu shine rikicin manoma da makiyaya . yana faruwane sakamakom rashin bayanai da wayar da kan al'umma musamman akan burtali, wannan ya haifarda asarar rayuka da dukiya ga al'ummar saji



TANTANCE HANYOYIN SAMUN BAYANAI

Manyan hanyoyin samun bayanai a Saji sun haɗa da radiyo da talabijin da yanar gizo da jaridu da mujallu da tauraron Ɗan'Adam da shela da wayar tafi-da-gidanka da tattaunawa da kuma tarurruka. A wasu lokutan akan yaɗa bayanai a wuraren raɗin suna ko ɗaurin aure da kuma cibiyoyin addini da ke Unguwar.

Wayar tarho da tattaunawa fuska da fuska hanyoyi ne da al'ummar Saji suke isar da saƙonni ga takwarorinsu na wasu unguwannin.

Zanen ya fitar da mutane da cibiyoyi waɗanda suke da ikon warware al'amari ko matsalar da aka gano.

Majalisar Jiha da Kwamitin Ilimi na Majalisar suna da tasiri da ƙarfin ikon kawo canji da kuma haɓaka kayayyakin koyo da koyarwa a fannin ilimi ga al'ummar unguwar. Hakan yana da alaƙa da Ma'aikatar Ilimi a matakin jiha da SUBEB da KSSSB da kuma KERD a matakin ƙaramar hukumar da garin Saji.

Ma'aikatar Ilimi ma tana da tasiri sosai da kuma kyakkyawar alaƙa da Kwamitocin Ilimi Majalisun Jiha da Tarayya. Ita ma ƙaramar hukuma da Majalisar Jiha suna da kwatankwacin irin wannan tasirin. Haka shi ma Dagaci da Kansila suna da tasirin kawo canji iri ɗaya, sannan suna da alaƙa ta kurkusa da gari saji da sakataren Ilimi na ƙaramar hukumar da kuma shugaban hukuma.

Tasirin Maiunguwa da masu tallfawa da shugaban ƙungiyar iyaye da malamai mai yawa ce, kuma suna da kusanci da garin Saji, kuma suna miƙa rahoton ayyukansu ne kai tsaye ga Dagaci hukumar ilimi. Akwai mutane masu tarin yawa waɗanda suke taimakawa kai tsaye ko ta gefe wajen ciyar da ilimi gaba. Suna da matsakaicin tasirin kawo canji saboda suna da alaƙa sosai da 'yan majalisar wakilai ta jiha da ta ƙasa. Haka kuma, suna da alaƙa da yankin ƙwarai da gaske.



TANTANCE HADURA DAKE BARAZANE NE GA JAMA'AR SAJI

Tantance haɗuran hanya ce ta gano da auna da kuma jera haduranda ke fuskantar garin sajidaki-daki. Bugu daƙari, an gano haɗurada ke yiwa Saji barazana. An yi amfani da jadawalin tantancewa wajen tattauna sabubban da suka haddasa su tare da tasirinsu.





- An yi amfani da salon tantance cibiyoyi da mutanen da za su iyabayar da tallafi domin gano waɗanda za su iya hoɓɓasa kuma suke da ikon kawo canji ga abubuwan da garin ke buƙata.
- An yi amfani da tsarin zane naƁenn domin a tantance matakin tasirin da cibiyoyi da mutanen da za su iya taimakawa da alaƙarsu da garin.
- An yi amfani da salon yanar-gizo wajen tantance haƙƙin mata.
- Tsarin tantance matsaloli ya fitar da abubuwa daban-daban da ka iya cutar da garin.
- Zanen hanyoyin sadarwa ya tantance hanyoyin da al'ummar garinke isar da saƙo tsakaninsu da tsakaninsu da sauran garuruwa da waɗanda za su iya bayar da gudummawa. A ƙoƙarin aiwatar da tantance abubuwa daban-daban, an tattauna da kowa da kowa, an tattauna a ƙungiyance don a yi tambayoyi da kuma yin bincike mai zurfi domin a samu tantancewa mai inganci.

CIKAKKEN BAYANI GAME DA GARIN SAJI

| | |
|---|---|
| Sunana Garin: | Saji |
| Karamar Hukuma: | Rano |
| Jiha: | Kano |

Adadin Al'umma: 3,500 Kiyasin(Maza 1603 Mata 1897)
Kiyasin Magidanta a garin 1950, 48 mata magidanta andDattijai magidanta1902

## Ajujuwan Shekarun Al'ummar garin Saji

| | |
|---|---|
| 0 5: Shekara Biyar Zuwa Kasa | 555 |
| Shekara 6 Zuwa 10: | 647 |
| Shekara 11 Zuwa 18: | 1,020 |
| Shekara 19 Zuwa 30: | 621 |
| Shekara 31 Zuwa 40: | 304 |
| Shekara 41 Zuwa 50: | 131 |
| Shekara 51 Zuwa 60: | 99 |
| Shekara 61 Zuwa 70: | 60 |
| Shekara 70 Zuwa Sama: | 63 |
| ADADI | **3,500** |

Manyan sana'oi Aikin yi:Nama da Kiwo, aikatan Gwamnati da ƙananan 'Yan Kasuwa

Kayayyakin da aka fi sayarwa: Kayayyakin masarufi da kayayyakin abinci da sauran kayan Masarufi

Kuɗaɗen da ke shigowa/Kuɗaɗen da ake kashewa

Matsakaicin abin da ke shigowa mutum a shekara: ₦200, 000

Matsakaicin abin da mutum yake kashewa a shekara:₦350, 000

Matsakaicin abin da ma'aikaci yake samu a kullum: ₦400, 000


Matsakaicin abin da ma'aikaci yake kashewa a shekara: ₦470, 000

Kiwan lafiya a Saji

Garin Saji suna cibiyar kula da lafiya mai tazar 6 KM ( kimanin tafiyar Awa 2 a ƙafa). Babu wadatattaun Horarun ma'aikatan lafiya a garin, akasari suna tafiya asibitin Rano ne don kiwan lafiya, Saboda haka idan barkewar annoba ta abkusuna fuskantar waha sosai, kuma wanda matsalar tafi shafa sune mata masu ciki da ƙananan yara, Mafi yawa mata suna haihuwane a gida suna amfani da ungozomomi na gargajiya. Idan kuma haihuwa tazo da matsala suna garzayawa zuwa babban Asibitin Rano kuma kawo yanzu babu wani ƙwaƙƙwarn canji na cigaba a harka lafiya a Saji kimanin shekaru uku baya



KUNDIN SAMAR DA TSARIN CIGABAN GARIN SAJI 2016




## WAXANDA ZA SU IYA TALLAFAWA

Bayan an gano matsalolin da ke addabar Saji na Rashin hanyoyin sadarwa na wayar hannu GSM a matsayin babban ƙalubalen da yake fuskantar Saji, al'ummar yankin sun tattauna game da muhimman mutane da ƙungiyoyin da gudummawarsu za ta iya kai wa ga cimma burin da ake da shi na ɗaga darajar sadarwa duba da zaburarwa da matakinsu na kawo canji. Sun kuma tattauna kan Mmatalar Ilimi; rashin Ajujuwan manya, buƙatar samar da malamai da ajujuwan Islamiyya da Karancin filin gina gidaje da gina hanyar Rano zuwa Saji zuwa Sayaya (hanyar tana buƙatar gyara

An fitar da masu tallafa wa al'umma da shugabannin al'umma da shugaban ƙaramar hukumar Rano da kwamishinan ilimi dana ayyuka da gidaje da ɗan majalisa da masu riƙe da sarautun gargajiya a matsayin muhimman mutanen da ke da ƙumbar susa.

## CIBIYOYINDA ZA SU IYA TALLAFAWA

A matakin hukumomi kuwa, ma'aikatar, ilimi da hukumar kula da makarantun sakandare da hukumar ilimi bai-ɗaya (SUBEB),kwamitin ilimi na majalisar jiha,da ma'aikatar ilimi ta tarayya da kamfanin sadarwa na, GLO MTN, NCCand Ma'aikatar Kananan hukumoni Duba jadawali na ƙasa da ya yi bayani dalla-dalla,




TANTANCE KARFIN IKON KAWO CANGI

An yi amfani da tsarin zane na Venn domin gudanar da wannan tantancewar. Haka kuma an yi amfani da tsarin zanen Venn domin tantance matakin ƙarfin ikodayake ko ikon da wani mutum ko wata ƙungiyoyi Ke da shi da kuma alaƙarsu da juna game da Cigaban Saji.






# ILIMI

### Saji suna da Firamare daya da qaramar sakandire daya

| | | | |
|---|---|---|---|
| Adadin yaran da suka shiga makaranta: **272** | Adadin Yara Maza: 24 | Adadin Yara Mata: 44 | Adadin 'yan ƙasa da shekara 5: 13 |
| | Adadin yara 'yan shekaru 6 zuwa 10: 21 | Adadin 'yan shekaru 11 zuwa 15: 25 | Adadin 'yan shekaru 16 zuwa 20 (idan ana buƙata): 09 |
| Adadin waɗanda suka kammala firamare: **2416** | | | Adadin Maza: 115 |
| | | | Adadin Mata: 301 |
| Adadin waɗanda suka kammala sakandare a Unguwar: **339** | | | Adadin Maza: 219 |
| | | | Adadin Mata: 120 |
| Adadin waɗanda suka kammala makarantar gaba da Sakandare: **215** | | | Adadin Maza: 178 |
| | | | Adadin Mata: 45 |
| Adadin waɗanda ba su taɓa zuwa makaranta ba**156** | | | Adadin Maza: 706 |
| | | | Adadin Mata: 800 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa makarantar Firamare: 667 | | | Adadin Maza: 375 |
| | | | Adadin Mata: 292 |
| Adadin yaran da suka daina zuwa makarantar Sakandare: 304 | | | Adadin Maza: 180 |
| | | | Adadin Mata: 124 |

***Adadin Masu bu**qata ta musamman**: 140***




TARIHIN GARIN SAJI

Saji Gari ne daga cikin garuruwan Karamar hukumar Rano a Jihar Kano. Garin yana da kimanin nisan 6 KM daga garin Rano, helkwatar, Saji ta kasance tuni tun kafin samar da Rano amman ta kasan cee koma baya wanda Cigaban ta Bai kai ya kawo ba, garin yana da Masallaci na zamani, Makarantar firanare da karamar secondary wadda suke amfani da wasu ajujuwan dake Firamaren kuma suna amfani da haraba daya ne. Saji nada karamar cibiyarkula da lafiya.

Mutanen garin Saji suna girmama junan su sosai, da manyan su musamman shuwagabannin su. Kauyen Saji yana tsakainin duwasu ne da suka kewaye shi da tsaunika, hanyar shiga garin na tsakanin wasu manyan duwatsune.

Alummar Saji banda noma babu wani kasuwanci mai karki da suka dogara da shi sai kiwon dabbobi, kuma yakasance suna fuskantar matsala ta gurin noma da muhalli wato filin gina gidaje saboda cigaba da ƙaruwa da ake samu nay au da kullungashi kuma garin a kewaye yake da duwatsu. Saji garin manomane da ma'aikata da ƙananan yankasuwa, suna da masu ilimi na addini da na zamani, a gargajiyance Saji suna ƙarƙashin masarautar Rano ne. duk da tsohon tarihi da garin yake dashi har yanzu saji tana da matsalolin na ƙarancin ruwan sha, da matsalar karyewar dam wanda yanzu ba a amfani dashi, wanda da za'a gyarashi zai samarda ayyukan yi ga al'ummar saji masu yawa kuma zai samar hanyar samun ruwan shag a jama'a, Shi Dam din za a iya noman rani.

## TASWIRAR GARIN SAJI

An fara fitar da taswirar Saji ne ba tare da sanya wata alama ba sakamakon lokacin damuna. Amma duk da haka an gano albarkatu da ƙalubale da matsaloli iri-iri da ke addabarta domin a ƙarfafi gwiwar al'umma su tattaunawa sosai domin samun mafita. A lokacin aikin, an gano albarkar ɗan'Adam da Allah Ya yi wa yankin da albarkatu Dam da Dawatsu, da abubuwan da kan sa walwalar al'umma da kuma harkokin da ake aiwatarwa cikin garin.

Bugu da ƙari, garin Saji yana da makaranta da gwamnati ta gina da ake yin karatun firamare da na ƙaramar sakandire a haɗe. Akwai ɗalibai maza da mata a makarantar da suke ɗaukar darussa a ajujuwan daban-daban.

Jama'ar SajiMusulmaine mafi yawansu sun dogara da manoma; Saji na da dajiwanda sukan yi farauta a ciki, abinda sukafi nomawa ya haɗarda masara, dawa, gero rake da rogo, barkono.







## KUNGIYOYI DA MUTANEN DA ZA SU IYA TALLAFAW

Abubuwan da suka taso daga bishiyar matsaloli, an yi nazarin ƙungiyoyi da mutanen da za su iya bayar da gudummawa wajen warware matsaloli. Al'ummar Saji sun fitar da muhimman mutanen da suke da zarafin tallafawa domin samar da canjin da ake fata a garin.

| Abubuwan da aka Gano | Waɗanda za su Iya Tallafawa | Cibiyoyi | Manyan buƙatu/ zaburarwa domin kawo canji | Karfin ikon kawo chanji |
|---|---|---|---|---|
| Rashin hanyoyin sadarwa na wayar hannu GSM | 1.Mai unguwa<br>2.Imam<br>3.Wakilin Dagachi<br>4.Haladu Saji<br>5.A.Yahuza<br>6.Rabiu Muhd<br>7. Alh Auwalu Saji<br>8.Zainab idris<br>9. Councilor<br>10. Shugaban ƙaramar hukumar Rano<br>11. Ɗanmajalissar Tarayya<br>12.Sanatar<br>13.Kwamishinan Kananan Hukumomi<br>14. Lamido Saji<br>15. AA Rano<br>16. Alasan Sule | 1.Majalisar ƙaramar hukumar Rano<br>2. Ma'aikatar Ilimi<br>3. Rano LEA<br>4. Ma'aikatar Kasa da safiyo<br>5. MTN /Airtel Kano head offices<br>6. NCC (Nigeria Communication Commission)<br>7.Kwamitin ayyuka da gidaje na Majalissar Kano | 1.Don kawo cigaba<br>2.Don kawo cigaba<br>3.Don kawo cigaba<br>4.Don kawo cigaba<br>5.Don kawo cigaba<br>6.Don kawo cigaba<br>7.Don kawo cigaba<br>8.Don Siyasa<br>9.Don Siyasa<br>10.Don Siyasa<br>11.Don Siyasa<br>12.Don Siyasa<br>13.Don kawo cigaba<br>14.Don kawo cigaba<br>15.Don kawo cigaba | 1. Matsakaici<br>2. Matsakaici<br>3. Matsakaici<br>4.Karamar dama<br>5. Karamar dama<br>6. Karamar dama<br>7. Karamar dama<br>8. Matsakaici<br>9.Babbar Dama<br>10. Babbar Dama<br>11. Babbar Dama<br>12. Babbar Dama<br>13. Karamar dama<br>14. Babbar Dama<br>15. Karamar dama |
| Ilimi; Ajujuwan manya, buƙatar samar da malamai da ajujuwan Islamiyya | | | | |
| Karancin filin gina gidaje da gina hanyar Rano zuwa Saji zuwa Sayaya (hanyar tana buƙatar gyara) | | | | |

# BISHIYAR TANTANCE MATSALA TA GARIN SAJI









Garin nada ƙaramar kasuwa dake ci da dare.

Akwai ƙaramar cibiyar kula da lafiya (sha ka tafi) a cikin garin, suna majalissu na hira na matasa da dattijai da yara da jama'a kan hadu su tattauna matsaloloin su da saura abubuwan daya damesu. Hoton dake biye taswirar saji ne dake nuna albarkatu da kuma ababan more rayuwa.Kuma zanen yana nuna fatan da Saji so ta zama a nan gaba wajen samu kayan more rayuwa.




***Taswirar Garin Saji***



*Figure: Lokaci Samar da Taswirar*



*Alummar Saji na Tabbatar da Taswira*








**Mazan garin Sajiyayin fitar da jerin Matsaloili Bi da Bi**

## Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli

Bishiyar matsaloli ta taimaka wajen tantance manyan matsalolin da ke addabar garin. Bishiyar hoto ne da ke nuna dangantaka tsakanin abubuwan da suka haddasa matsalolin da kuma tasirinsu. Bishiyar matsaloli tana buɗe ƙofar shiga tsakani tun daga tushen abubuwan da suka janyo ta da zummar warwarewa. Gangar jikin matsalar, kamar yadda aka nuna, ita ce Rashin hanyoyin sadarwa na wayar hannu GSM (babu abin kai sabis da masu waya a garin zasuyi amfani da shi wand yana shafar tattalin arzikin su da sauran hakokin su). Abubuwan da suka haddasa matsalolin da tasirinsu, kamar yadda aka tattauna da al'ummar Saji, an nuna a bishiyar matsaloli da ke biye.



RANKING — Rano Central Community — 08-11-15

| Issues | Women | Children | Men | Total | Rank |
|---|---|---|---|---|---|
| 1 Drainage | 0 9th | 0 | 6 9th | 06 | 9th |
| 2 Road | 20 3rd | 05 4th | 78 1st | 103 | 2nd |
| 3 Lack of Portable Water | 28 2nd | 15 3rd | 61 3rd | 104 | 1st |
| 4 Lack of Electricity | 10 5th | 0 | 52 4th | 62 | 5th |
| 5 Unemployment | 7th 07 | 0 | 74 2nd | 81 | 4th |
| 6 Education | 5th 10 | 33 2nd | 19 7th | 62 | 5th |
| 7 Health | 30 1st | 40 1st | 17 8th | 87 | 3rd |
| 8 PWD Empowerment | 7th 07 | 0 | 21 6th | 28 | 8th |
| 9 Drug Abuse | 19 4th | 0 | 24 5th | 43 | 7th |




**Matan Garin Sajiyayin Fitar Da Matsaloli Bi Da Abi**








*Taswirar Garin Saji*



## YANAYIN ZAMANTAKEWA

Sajiƙauye ne dake da yaan alumma kimanin kamar yadda suka ƙiyasta31,188 (18,783 maza da 12,405 mata). Babu wata ƙididdiga data nuna rabe-raben jagoranci cikin iyalina magidanta arubuce. Ajin yara ya shekara biyar zuwa ƙasa su sukafi yawa).

Bugu da ƙari, mutanen garin Saji community mafiyawansu manomane, da sana'oin hannu,kasuwanci da yan ƙalilan ma'aikatan gwamnati, Kowane magidanci yana samun aƙalla Naira 325, 000 a shekara, sannan yakan kashe kimanin Naira 430, 500 (a ƙiyasin albashin ma'aikata). Mutane sun mallaki rumfunan kasuwanci.a unguwar. Jama'ar garin sukan kashe matsakaicin abin da suke da shi.Haka kuma, garin nada masu ƙananan sana'o'i waɗanda suke samun tsakanin Naira 1,000 zuwa 1,500 a rana.




## LAFIYA

Garin Sajiyana da ƙaramar cibiyoyin kula da lafiya aman basu da wajen sayen magani (chemist) ko asibiti mai zaman kansa. Shekarun baya kauyen sun hadu da kamuwar wasu Cututtuka kamar su kwalara, maleriya, tifod, sabodarashin tsaftatattcen muhalli da kuma kyakyawan ruwan sha.Cibiyar kula da lafiya bata da yalwar da zata iya kwantar da mara lafiya, mafiyawan masu zuwa cibiyar matane, kuma babu wadatattun kwararrun ma'aikata, saji suna da unguwar-zoma masu karbar haihuwa. Babban halin da cibiyar kula da lafiyar Saji a yanzu shine babu wajen kwanciya da kuma ma'aikatan lafiya.



## ILIMI

Anyi bayanin makarantun dake saji a sama. Makarantar bata da wadatattun ajujuwa, da malamai da ofishin zama na malamai, kuma makarantar tana fuskatar matsalar ruwan sha musamman saboda dalibai. Saboda matsalar ta ƙarancin ajujuwa, ya tilastawa hukumar makarantar yin amfani da ƙarƙashin bishiya a matsayin aji do horar da dalibai, kuma daliban suna zamane a ƙasa don daukar darasi.

Domin tantance ingancin ilimi a SAji, an yi amfani da kundin da yake ɗauke da hakkokin ciyar da ɗalibi gaba (Promoting Rights in School Charter). Hakkin ciyar da ilimigaba a makarantu ya ta'allaƙa kan haƙƙoƙi guda goma da aka rairayo daga Tsarin Shari'a na ƙasa (National Legal Instruments) (watau kamar kundin tsarin mulki da yarjejeniyar haƙƙoƙin ɗan'Adam na ƙasa da ƙasa).

An yi amfani da shirin PRS domin tantance haƙƙoƙin ilimi a unguwar. Manufar da PRS ke son ya cimma ita ce shigo da al'ummar kasa domin tabbatar da ilimi mai inganci sannan a gane fahimtar 'yan kasa a wuraren da suke rayuwa inda. A tsarin, lamba 1 ce mafi karanci, 5 kuma lamba mafi girma. Ga haƙƙoƙin:






-na ɗaya da ba biyu. Matsala ta uku shine Karancin filin gina gidaje da kuma Karancin Ruwan sha mataki na huɗu. Tasirinsu yana addabar garin ƙwarai da gaske.

Haka kuma, akwai ƙalubalen Lafiya: Buƙatar ɗaukaka ko faɗaɗacibiyoyin lafiya da sake gina hanyar Rano zuwa Saji zuwa Sayaya (hanyar tana buƙatar gyara. Waɗannan matsaloli sun samu ne sakamakon rashin aikin yi a tsakanin matasa da rashin samun damar cigaba da karatu da kuma gazawar hukumomin tsaro. Bugu da ƙari, akwai ƙarancin Lantarki ( Mayar da durakun wuta da kayan lantarki da suka karye. Alummar sun tattauna buƙatarsu ta gyaran dam wanda in har an gyara shi zasu sami ayyukan yi da cigaba kuma garin zai bunƙasa soasai.

Waɗannan matsaloli sun haifar da ƙalubalen gurɓacewar sosai ga matasan garin Saji wand aka iya haifar da shaye-shayen miyagun ƙwayoyi.

Sassauƙar Hanyar Jera Matsaloli Garin Saji Bi da Bi

| Lamba | Al'amari (Buƙatu) | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|---|
| **1.** | Karancin filin gina Gidaje | 66 | 11 | 12 | 89 | **3rd** |
| **2.** | Gina hanyar Rano zuwa Saji zuwa Sayaya (hanyar tana buƙatar gyara) | 28 | 05 | 14 | 47 | **6th** |
| **3.** | Ilimi; Ajujuwan manya, buƙatar samar da Malamai da Ajujuwan Islamiyya | 60 | 08 | 34 | 103 | **2nd** |
| **4.** | Rashin Hanyoyin Sadarwa na Wayar Hannu GSM | 105 | 44 | 28 | 177 | **1st** |
| **5.** | Karancin Ruwan sha | 41 | 14 | 26 | 81 | **4th** |
| **6.** | Lafiya: Buƙatar ɗaukaka ko faɗaɗa Cibiyoyin Lafiya | 18 | 08 | 34 | 60 | **5th** |
| **7.** | Tsada da Karancin Takin Noma( Gyara ko sake gina Dam na Saji Dam domin Noman Rani) | 15 | 08 | 04 | 27 | **9th** |
| **8.** | Lantarki ( Mayar da Durakun Wuta da Kayan Lantarki da suka Karye) | 20 | 06 | 03 | 29 | **7th** |
| **9.** | Aikin yi | 15 | 05 | 09 | 29 | **7th** |



## KALUBALEN DA KE FUSKANTAR GARIN SAJI A HALIN YANZU

Sanin kowane babu wata alumma da bata fuskantar wani ƙalubale ko wacan. Kamar Saji, Shekaru da dyawa akai watsi da ita wajen wanda ya haifar da matsalolin da suke ciki, hakan ya shafi yanayin ci gaban su bama ayanzuba har nan gabaa yaya alummar saji zata kasance. Garin a halin yanzu na fuskantar matsalar ina makomar su nan gaba.

Akwai matsalar rashi aikin yi sana'oi musamman ga matasa, wanda ya haifar da shaye shayen kwayoyi da lalacewar tarbiya ga wasu matasan. Akwai fadace fadace tsakanin manoma da makiyaya a wani lokacin gami da ƙarin rashin ingantatccen tsaro dake barazana ga Saji da ka iya haifar da rasa rayuka da dukiyoyi.

Sanna Yanayin Garin a wajen rashin gina muhalli, da rashin ingantacciyar hanyar da hanyar Sadarwabugu da ƙarin haɗari rashin lantarki da ingantaccen ruwan sha sun ƙara sanya garin saji cikin mawuyacin hali wanda ya tallafa wajen ƙaruwar yaduwar cututtuka cikin sauri irin su taifot da kwalara.

Rashin isassun kayan kua da lafiya ya ƙarawa Alummar saji matsalolin gaske wanda sai sun kasha kuɗi sosai wajen tafiya samo maganin da kuma war ware wasu ƙalubalen nasu.

Bayan fitar da Jera Matsalolin Saji bi da bi ta Sassauƙar Hanya,garin Saji yana fuskantar Matsalar Karancin hanyar sadarwa ta wayar ta hannu shine babban ƙalubale wanda zai inganta tattalin arzikin garin da samun bayanen kan kiwan lafiya, haka kuma Matsalar Ilimi na rashin ajujuwan manya da buƙatar samar da malamai da ajujuwan Islamiyya ke kawo tarnaƙi ga cigaban garin. Waɗannan matsalolin a jera suke a mataki-





| S/N | Yarjejeniyar PRS | Tantancewa (1 mafi ƙaranci, 5 mafi girma) |
|---|---|---|
| 1. | Haƙƙin samun kyakkyawan ilimi kuma kyauta | 1 |
| 2. | Haƙƙin rashin nuna wariya | 2 |
| 3. | Haƙƙin samar da isassun kayayyakin more rayuwa | 1 |
| 4. | Haƙƙin samar da wajen zama mara haɗari | 3 |
| 5. | Haƙƙin samar da ƙwararrun malamai | 3 |
| 6. | Haƙƙin samar da tsarin koyarwar da ya dace | 2 |
| 7. | Haƙƙin sanin 'yancin kai | 2 |
| 8. | Haƙƙin a dama da mutum a wajen ɗaukar mataki | 2 |
| 9. | Haƙƙin samar da makaranta mara ƙunbiya-ƙunbiya | 2 |
| 10. | Haƙƙin samar da ingantacciyar koyarwa | 4 |

Jadawali na sama yana nuni da cewa alummar saji ba sa shiga a dama da su a wajen ɗaukar mataki kan wani abu da ya shafi al'umma. Haka kuma basa samun isassun kayayyakin more rayuwa, sannan ga tauye musu haƙƙi na samun ingantacce kuma kyakkyawan ilimi kyauta da kuma haƙƙin samar musu da ingantacciyar koyarwa. Kuma suna buƙatar a tattauna da su wajen samar da jadawali ilimin da ya dace da yankinsu

## JUYAWAR YANAYIN

Garin Saji tana da yanayi iri biyu; rani da damina.Ana samun yanayin rani ne daga Disamba zuwa Yuni.Damina kuwa tana farawa daga watan Mayu, inda ruwa yakan kankama tsakanin Agusta da Satumba. Jihar Kano kacokan ta fi samun yanayin zafi da yawa, ruwan sama(watau damina) yawanci akan same shi ne a watannin Mayu da Yuni da Yuli da Agusta da kuma Satumba. Kano na samun rani a watannin Janairu da Fabrairu da Agusta. Akan samu matsakaicin zafi a watan Afrilu, yayin da sanyi ya fi tsananta a watan Agusta. Satumba shi ne watan da aka fi samun ruwan sama, haka kuma Janairu ne watan da rani ya fi ƙamari. Ayyukan noma a garin ba shi da yawa sosai sannan kuma ba na kasuwanci ba ne. Mutane a Saji suna fara shirye-shiryen shuka a tsakanin Fabrairu da Maris. Jadawalin da ke biye yana nuna yadda yanayin ya karkasu da kuma yadda ayyukan suke gudana a tsakanin waɗannan lokutan.




## YANAYIN SAJI TSAWON SHEKARA

| S/N | Yanayi | Janairu | Fabrairu | Maris | Afrilu | Mayu | Yuni | Yuli | Agusta | Satumba | Oktoba | Nuwamba | Disamba |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Nama Damuna | L | L | L | L | H | H | H | VH | VH | L | L | L |
| 2. | Kiwan | L | L | L | L | H | H | H | H | H | H | H | H |
| 3. | Noman Rani | L | L | H | H | H | L | L | L | L | L | L | L |
| 4. | Aikin Kafinta | H | L | L | L | L | L | L | L | L | H | H | H |
| 5. | Sana'ar Dinki | H | L | L | L | L | L | L | L | L | H | H | H |
| 6. | Cutar kwalara | L | L | L | L | H | H | H | H | H | L | L | L |
| 7. | Cutar Kyanda | L | L | L | L | L | L | L | L | H | H | H | L |

Karin haske: VH ƙwarai da Gaske H ƙwarai M Matsakaici L ƙasa VL ƙasa Sosai

| Lokuta | Aikace aikacen MazaSaji na Kullun Safe zuwa Dare |
|---|---|
| 5:00 am -8:00am<br><br>8:00am 1:00am | Sallar Asuba, aci abincin safe,wanka, gaida manya, duba iyali, halartar daurin aure da suna in da akwai Gona, kiwo, kasuwa gay an kasuwa da kuma masu tafiya wajen aiki ga ma'aikatan daban daban |
| 1:00am 4:00pm | Salar Rana, lokacin hutawa da cin abin rana |
| 4:00pm - 6:00pm | Yammacin aikin gona, Kwallo ga matasa, wasu na tafiya Islamiyya,<br>Masu ɗebo ruwa ko itacen girki nayi<br>Sai tarukan tattaunawa in da akwai |
| 6:00pm 10:00pm | Sallar magrib, aci abincin dare, Asaurari labarai, wasu na tafiya karatu addini na dare, Hira, Kallon Kwallon league, da masu zancen dare |
| 10:00pm-05:00pm | Lokacin baccin |





| Jihar /LRP | KANO | | | KARAMAR HUKUMA | KABO | | GARI | | GAMMO | |
|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|---|
| Rashin cancanta/ cancanta a samu (mata, yara, talakan da ba shi da fili ko rukunin jama'ar da aka gano) | Adadin waɗanda suka cancanci su samu a yankin da akayi shirin | | Al'amari | Abubuwan da suka haddasa | Haƙƙoƙin da aka tauye | Kundin tsarin mulki/ policy enterta -inment | Adadin waɗanda suka cancanci su samu damar da suke neman haƙƙinsu a farkon fara shirin | | Waɗanda nauyin yin aikin ya hau kansu | Sauran muhimman masu ruwa da tsaki |
| | Namiji | Mata | | | | | Namiji | Mata | | |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Filin gina gidan kwana | Rashin ingantaccen shugabanci da aiwatar da tsare tsare | 'Yancin sa mun ilimi | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | -Ma'aikatar Kasa da safiyo | -Masu gonaki |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Hanya | Rashin ingantaccen shugabanci a aiwatar da tsare tsaren Gwamnati Rashin ingantaccen Cigaba | 'Yancin ababan more rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | -Ma'aikatar ayyuka -kwamitin ayyuka da Gidaje | Kamfanonin gine gine da Ayyuka |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Rashin ingantacci yar hanyar sadarwa | Rashin ingantaccen shugabanci da aiwatar da tsare | 'Yancin ababan more rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | NCC | -Airtel -MTN -GLO -Etisalat |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Karancin Ruwa | Rashin ingantaccen shugabanci da aiwatar da tsare tsare | 'Yancin ababan more rayuwa ingantattu | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | Ma'aikatar ruwa | Masu tallafawa na gari |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Kiwan Lafiya | Rashin ingantaccen shugabanci da aiwatar da tsare tsare | Haƙƙin samun ingantattun kayayyakin kula da lafiya | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | Ma'aikatar Lafiya | -NGOs -LHC |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Noma | Rashin ingantaccen shugabanci da aiwatar da tsare tsare | 'Yancin ababan more rayuwa ingantattu | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | Ma'aikatar Noma | NGOs |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Lantarki | Rashin ingantaccen shugabanci da aiwatar da tsaretsare | 'Yancin ababan more rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | -Ma'aikatar samar da lantarki a Kauyuka ta jiha -KEDCO | NGOs -NGOs |
| Maza, Mata, Matasa da Yara | 1,603 | 1,897 | Aikin yi | -Rashin ingantaccen shugabanci -Rashin cikakkun bayanai | Haƙƙin samun ingantacciyar rayuwa | Kundun Tsarin Mulkin Najeriya | 1,603 | 1,897 | -Ma'aikatar ayyuka -Ofishin shugaban ma'aikata - Majalissar Karamar hukumar Rano | - A A rano - HOD Agric Rano (Irrigation) |

Take Haƙƙoƙin

An lissafa haƙƙoƙi ne domin a gano yadda ake tauye 'yancin jama'a alummar agarin Saji. An hana al'ummar Saji waɗannan haƙƙoƙi:

- Haƙƙin ingantaccen ilimi
- Haƙƙin ingantattun ababen more rayuwa (Lafiya)
- Haƙƙin ingantattun ababen more rayuwa (ruwan sha da aikin gona)
- Haƙƙin jin daɗin zamantakewa (Rashin aikin yi noman rani)
- Haƙƙin ingantattun kayan kiwan lafiya
- Haƙƙin ingantattun ababen more rayuwa ( lantarki da filin gina gida)

Take waɗannan haƙƙoƙi ya taimaka ƙwarai da gaske wajen tauyewa tare da rage yin rayuwa mai inganci a yankin. Rashin ingantacce ilimi shi ma wani ƙalubale ne sakamakon rashin ƙwararrun malamai da ƙarancin kayayyakin koyo da koyarwa a makarantu.Bugu da ƙari akwai tauye haƙƙin na rashi aikin yi wande da akwai damar samar da Dam da za aiya aikin noman rani da damuna. Haka tauye hakkin ababan more rayuwa na lantarki da sadarwa ya taimaka wajen rashin samar da bayanai da ka iya wayar dakai da kuma samun sabbin bayanai na cigaba.







| Lokuta | Aikace aikacen Mata Saji na Kullun safe zuwa dare |
|---|---|
| 5:00 am - 5:30 am | Lokaci Salla Asuba |
| 5:30am 8:00am | Gyaran gidawanke kwanke, share-share, Pshirya abincin safe da shiryawa yara zuwa makarantar safe da shirye-shiryen kayan cinikinsu |
| 8:00am - 12:00pm | Wankin kaya, wasu suna hutawa, wasu suna karatun Littafan Hausa |
| 12:00am 2:00pm | Shirya abincin rana, Sallar Rana da cin abinci |
| 2:30pm 4:00pm | Subaiwa Yaran su Abinci Sannan Su kai su Islamiyya |
| 4:00pm -6:00pm | Share gida da Sallar Yamma |
| 6:00pm 7:00pm | Shirya abincin Dare wanka |
| 7:00pm 10:00pm | Duba aikin da akaba yara a makaranta, wasu suna tafiya wajen hidimay yan uwa indan akwai, Sallar dare, Kallon TB, tattaunawa da iyali, ha Hira |
| 10:00 na Dare | Lokacin Bacci |

| Lokuta | Aikace aikacen Yara Saji na Kullun safe zuwa dare |
|---|---|
| 6:00 am - 8:00 am | Sallah , gaida iyaye, halarta makarantar Kur'anic , Karin kumallo wanka da tafiya talla |
| 8:00am 1:00pm | Tafiya Makarantar boko da Islamiyya, wasu kuma suna ɗaukar talla, ko su tafi gona da samo ciyawa |
| 1:00pm - 2:00pm | Lokacin Salla da cin abincin rana wasu na tafiya makarantun islamiyya, ko kasuwa, wasu na share share da gyaran gida da taimakawa iyaye |
| 2:00pm 4:00pm | Sallar rana, waka, da taimakawa iyaye da zuwa cefane |
| 4:00pm 6:00pm | Suna tafiyya Islamiyya wasu na taimakawa iayen su aikace aikacen gida |
| 6:00pm -10:00pm | Sallar yamma, Cin abincin dare tafiya Islamiyya wasu na was anni |
| 10:00pm- 6:00am | Lokacin Bacci |

***Figure 2Aikace aikacen Jama'ar Saji nayau da Kullun***








Ma'aunin {A Kasa A Fai Fai} na Maza da Mata

| Ɓangare | Sakamakon (Mata) | Sakamako (Maza) |
|---|---|---|
| Shugabanci | 1 | 1 |
| Samun kuɗin shiga | 5 | 4 |
| Kula da gida | 1 | 3 |
| Mallakar Kadarori | 1 | 1 |
| Tsaro | 5 | 5 |
| Samun damar ilimi | 1 | 2 |
| Ɗaukar matsaya a al'amuran al'umma | 3 | 3 |
| Damar samun iko | 3 | 3 |
| Shiga al'amuran al'umma | 3 | 2 |
| Aikin yi | 2 | 1 |




TANTANCE HAKKOKI


Jadawalin na nuna tazarar da ke tsakanin maza da mata a lokacin aikin tantance haƙƙin mata. Akwai daidaiton ra'ayina kurkusa da ratar da aka samu a tsakaninsu, wanda yake nuna cewa al'ummar unguwar sun fahimci banbancin da ke tsakanin maza da mata.

A Saji, mata ba sa taka kowace irin rawa a fannin shugabanci da shiga a dama da su cikin al'amuran jama'a. Amma duk da wannan, matan yankin suna da kazar-kazar duk da cewa ƙalilan ne ke shiga harkokin ɗaukar wata matsaya da ta shafi al'umma. Suna da 'yancin bayar da gudummawa a al'amuran tattalin arziƙi, amma ban da na siyasa. An amince da cewa mata suna da haƙƙin samun ilimi, amma ayyukansu sun fi ga kula da gida.

bakinsu yayin a ɗaukar wata matsaya kan wani al'amari da ba su muƙamai da kuma ba su damar bayar da irin tasu gudummawar a al'amuran al'umma.

A garin Saji, mata suna da taƙaitaccen 'yancin samun ilimi; watau a ƙarfafa musu gwiwa su shiga makaranta. Har yanzu akwai adadi mai yawa na matan da aka cire daga makaranta a dalilin za a yi musu auren wuri da sauran dalilai na gazawar iyaye wajen ɗaukar nauyin karatun nasu da makamanta haka  Rashi wadatattaun ajujuwa ya dada hassada rashin ilimin matan Saji saboda iyayen basu hakuri da su bari suje nesa da su.


An yi amfani tsarin a kasa afai-fai domin a nitsa sosai wajen tantance haƙƙoƙin mata. Aikin yana so ya auna yanayin zamantakewa da tattalin arziƙi da kuma siyasa domin a gano abubuwan da ke kawo tarnaƙi ga ci gaban mata ta yin amfani da abubuwa daban-daban a kan ma'auni na 1 zuwa 5; lamba 5 mafi girma, yayin da lamba1 kuma mafi ƙaranci.









## Aikace aikacen Mata da yaran Saji nay au da kullun




**Aikace Aikacen Maza Nayau Da Kullun A Saji**




## KADARORI


Kowane mutum mace ko namiji ko Iyali a garin Saji yana da 'yancin mallakar gona idan har akwai wadatattun filaye. Amma sakamakon bunƙasar iyali da aka yi ga duwatsu da suka kewaye Saji, sai ya zamana ragowar filin da ya rage wa garin ya haddasa raguwar samun damar kara gidaje da ƙananan harkokin kasuwanci kamar gina shagunan sayar da kayayyakin masarufi da ɗakunan sayar da magani da wuraren sayar da abinci da kuma wuraren hada-hadar motocin haya.



Mata lokacin tantance haƙƙokin mata








Haƙƙokin mata a fayyace




## TANTANCE HAKKOKIN MATA

'Yancin mata shi ne haƙƙoƙin aka keɓe musamman domin mata da 'yanmata a ƙasashen duniya masu yawa. A wasu wuraren, ire-iren waɗannan haƙƙoƙi an tabbatar da su ta hanyar yi musu doka da tsarin zamantakewar al'umma. A wasu Wuraren kuwa, a iya cewa an yi watsi da su. Lamuran da ake dangantawa da haƙƙin mata ba a taƙaita su ga 'yancin yin zaɓe ko taƙaita haihuwa ba kaɗai..

A Arewacin Najeriya, al'ada da addini suna ci gaba da taka muhimmiyar rawa a sha'anin 'yancin mata. An samu cigaba sosai a 'yancin mata musamman wajen faɗaɗa tattalin arziƙinsu da samun damar yin ilimi da kuma yadda suke shiga a dama da su a al'amuran al'umma. Duk da wannan ci gaban da aka samu, har yanzu akwai ƙalubale wajen sanya su cikin al'amuran shugabancin da jin ta